# GURBI A TAKAICE

Taikacin Sanfarin SadaRwa Domin Cigaban Jagora

**GURIN HARUFAN KAHKA NA GINUWAR JAGORA**

Dangance da sanfarinmu SadaRwa“KAHKH” jagora krista mai tsarki mutum ne wanda ya san Allah (Kristi), an horasda shi kuma yana rayuwa a cikin al’umma mai taimakawa da cikaken hali (Al’uma), yana da halin kirki (Hali), ya san nufin Allah, yana kuwa gabataswa da wannan nufin tare da inganci, haske da juyayi (Kira), kuma mutun ne wanda ke da kyawawan baye baye, hikima da husa’o’i domin jogarantan jama’a zuwa ga cikar wannan nufin (Hazaka), kuma yana girma cikin wadannan halaye a cikin rayuwarsa ta yau da kullum.




Mafi yawancin lokuta, a cikin bunkasarda jogara, mu kan fi buga kusa a kan harafi “H” na karshe, watau Hazaka. A lokacinda saurayi ko budurwa suka tafi karatun Litafi Mai Tsarki,me a ke duba? Hazaka! Mai yiyuwa akan kula da sauran sasan hudu, amma akasari abinda muke tunani dangance da “bunkasar jagora” shi ne hazakasa watau kwarewarsa a cikin sanin Litafi Mai Tsarki, yin wa’azi, bada shawara ko kuwa gargadi da dai sauransu. Hazaka nada tamani amma bata is aba ita kadai a cikin panonin ginarda cikakun jagorori masu tsarki. Shi ya a yau muna fama da “rashin cudanya” a cikin masu jagorinci.

Cigaba nada tamani kamar yadda hazaka ke da tamani, ama bai wadatas a tabatarda cewa rayuwar jagora ta bada sakamakon kyakyawan gurbi ko kuwa gado mai dorewa kawai ba. Masu jagoranci da dam aka iya gudanas da abubuwa da dama ama am aba tare da sun ci nasara ba. Dangance da binciken Robert Clinton 70 a cikin dari na jogorori wadanda su yi galaba sosai a cikin jagorancin bada kyakyawan gubi basu karewa da kyau. Wadansunsu kan faduwa a warwats, tare da aikata abin asha a bainin jama’a, a lokacinda shuwagabani da dama wadanda suka kasa bada gurbi na gari ke shudewa a cikin duhu. Su kan yi gajerar faduwa saboda a cikin rayuwarsu da mutane ke tunanin cewa akwai cigaba babu cudanya tsakanin bunkasarda jogaranci cikin hazaka da bunkasarda da jagoranci cikin halaya nigari. Rishin kyakyawan hali ya zama baban dalilin da yasa masu jagoranci ke kasa cika aikinsu tare dayin nasara, wannan rishin hali kuwa kan iya samo tushensa a cikin rishin Yesu da al’uma a cikin rayukan shugabani.
A bayannan, wani bincikenda aka gudanar a cikin kasashe 14 ya nuna cewa dalilan gawgawar dawowa mai zafi zuwa ga aikin mishinare (a cikin tsofofi da sabobin kasashe masu aikawa) basu da halaka da rishin inganci horo na farko da aka samu cikin aikin mishan. Wannan binciken ya nuna cewa wadanan dalilan sun shafi abubuwa da dama da ke kewaye da ruhaniya, halaya da cudanya da sauran jama’a a cikin rayuwar mishinare. Watau ba wai rishin kwarewa ko hazake ne ke raunanarda mishinare ba, amma rishin inganci da ke samu cikin sauran sassa da su kamata ba. Wadannan sassan kuwa ba a cika kula da sub a a cikin shirye shirye, sun kumshi – Kristi, Al’uma da Halaya (ba shaka wannan binciken bai Kira muhinanci na da ba haka ba da wannan pannin kira ya fito)
A cikin shanfarin manNewa, muna zance game de duk abinda ya shafi jagora, ba kansa kadai ba. Baban gurinmu shi ne kawo canji a cikin dukan sassan rayuwar shugabani domin yafa cikakiyar surar Yesu Kristi.

## MATAKAI HUDU DOMIN GINUWAR JAGORA MAI TSARKI

Idan mun yarda cewa Jagaranci mai tsarki a cikin kristanci ya kumshi dukan wadannan sassa biyar watau “KAHKH”, bai tsaya a hazakar karatu ba kawai, to lalle gina wannan shugaba mai tsarki na da saukin fada da baki fiye da aikatawa. Tura mutun a taruwa ko kuwa bada litafi a kan jagoranci a karanta shi kadai bai isa. Ginuwar jagora mawuyacin abu ne wanda mutane kalilan ne suka gane shi. Wannan ya sa a cikin mafi yawanci kungiyoyi ba a cika ba wannan al’amiri muhimanci ba. A kan bata lokaci a kan cacar baki ba tare da aikatawa ba. Karamin kokarinda ake kowowa a cikin ginarda masu jagoranci kadan ne kuma mara inganci bugu da kari bai kumshi pannoni da dama ba domin cigaba mai inganci a cikin rayuwar jogora. Bayan tura matasa a cikin makarantun Litafi Mai Tsarki, mu yi fatar wadanan jagora su cigaba su kansu. A lokacinda aka tambayi wanni jagora me husa’ar gina masu jagoranci ke nufi, sai ya ce : « ba abinda za a yi sai da a bari mai ya cika tukunya » watau yana nufin « bamu da ingantaciyar husa’a domin gina masu jagoranci, muna bagen al’amura su yi dadi ne kawai !»
A dalilin haka lokuta da dama, an fi bada kokari a panni darusa da koyaswa- watau ciki. Ba a sa lokaci isashe domin bunkasarda kyawawan matakai domin bunkasarwa wadanda suka kunshi yanayi da abinda ke ciki.
Husa’ar Yesu domin ginarda almajiransa na takaituwa a cikin Markus 3:

*Ya zabi goma sha biyu – ya kuwa zabi su zama manzanni – zasu zamna tare da Shi ya aike su wa’azin bishara atare da basu ikon fitar da aljanu.*

A cikin wannan furuci mai sauki amma kuma mai zurfi, mun gani dala dala yadda Yesu ya gina almajiransa. A takaice, Yesu a kafa *yanayi mai kawo canji* a kewayen masu jogaranci masu tashe.:

- Kewayen *ruhaniya*, wanda ya kumshi zumunta (da kansa, da Allah Uba kuma ta hanyar addu’a).
- Duniyar cudanya, wadda ta kumshi hulda da baban jogara da kuma, da kuma yin mu’amala da sauran jama’a (al’umar almajirai).
- Yanayi domin *koya*, wana ya kumshi ayyuka masu kallubalanta, wahala da zarafi da dama domin koya.

Kana a cikin yanayi mai kawo canji, ya koyarshe su – watau abinda ya kumshi cigaba.
A takaice, ga yadda Yesu ya gina almajiransa. Watau yanayi + abinda ke kumshe a ciki = matakan ginuwar cigaba.
Mun fi so a al’adance zu zaunarda masu jagoranci a cikin layuyuka a kan tebur tare da yi masu koyaswa mai tsawo a cikin kokarinmu na gginasu. Muna da karfi cikin sani amma raunana game da abinda ya shafi yanayinda mu ke kafawa domin cigaban masu jagoranci.

Akasari game da abinda ya shafi kirkiro husa’ar cigaban jagora mun fi bada karfi a kan koyaswa. Alhali kuwa wajibi ne mu bada karfiga sauran sasa hudu “na matakan canji”:

- Ruhaniya
- Hulda
- Zarafi domin koya
- Koyaswa

Haka ne rayuka suka canza. A duk lokacinda wadannan abubuwa hudu suka kasance a cikin shirin bunkasarwa, to rayuwa a cikin ruhaniya zata karfafa, hulda ta karfafa, za a ginarda halaya, kira zai tabatu kuma halin jagoranci zai ginu da kyau.

Wannan kuma wata dabi'a ce a cikin Ekklisiya ta farko:

*Suka kuwa lizima a cikin koyarwar manzanni da zumunta, da kuma kakarya gurasa da yin addu'a. (Ayyukan Manzanni 2:42)*

Suka lizima cikin wadannan abubuwa hudu:

- Koyarwar manzanni – karatu
- Zumunta – Hulda
- Kakarya gurasa – abinda ya shafi koya
- Addu'a – Ruhaniya

Marubucin shuwagabanin kristoci dari a cikin duniya, wadanda al'adunsu suka banbanta kwaran gaske wadannan tambayoyi, "Yaya a ka gina ka?

Me ya ja hankalinka tare da baka cikakiyar koyaswar zama jagora? Me ya sa ka zama jagora a yau?" Ko da yake tambayoyi sun banbanta, sun buga kusa kan panoni da suka shafi iyaye, bada kyakyawan gurbi, sha'awar jagoranci, kunci, matsayi, yadawa, rashin cin nassara, ayyuka masu kalunbalanta, da sauransu. Wani zai ambaci koyaswa, wadanda a lokacinda suke daukarta suna da shawa'ar halin malantakata da kuma abinda suke koya a duk lokacinda suka tuna

Wannan bai kamata ba ya bamu mamaki, saboda binciken Bishara ma ya bayana mana Yesu ma ya yi haka tare da Almajiransa. Husa'arsa ba wai ta tsaya kan koyaswa ba ne kawai, ama ya kafa kyakyawan yanayi mai kawo canji cikin ginuwar jagora wanda ya kumshi ruhaniya, hulda da zarafi domin koya.

Bai wai nuna son karyas da darajar koyaswa ba ne. I, lalle muke bukatar koyaswa mai zurfi; saboda kayaswa ta kasance daya daga cikin abubuwa hudu masu canji na sanfarin SadaRwa. Amma, idan aka buga kusa kanta ita kadai, ba iya wadataswa. Domin gina rayuka t wajibine mu shiryasda yanayi mai kawo canji wanda ke da karfi a pannin ruhaniya, hulda da zarafi domin koya ta hanyar aikatawa .

Karamin misali, mu dauki cewa muna son gina masu wa'azi. Ba mu iya tura su da farko a waje domin yiwa batatun tumaki bishara. « Ku je dai ku yi !» Ko za a ci nassara ? Ko za su koyi wani abu game da bishara? I, ba shaka!

Ya yanzu bari mu saka **pannin hulda**, ta wurin turasu waje tare da masu wa'azi wadanda suka kware, wadanda zasu lura dasu tare karfafasu da kuma kawo masu gyara.

A yanzu bari mu kara wani pani mai karfi kwaran gaske **na ruhaniya** ta wurin hada masu wa'azinmu da masu yi masu addu'a kafin su fara zuwa hilin daga. Za su yi addu'a da kuka domin batatu, tare da shiga cikin kofofin Allah da bakin cikin domin batatu marasa Yesu. Kanan, a lokacinda suka fita domin bishara, wajibi ne su nemi taimako daga Allah, tare da tambayar Sa a wurin wa za su je, tare da jira Ya saka masu datatun kalmominda za su furta. Haka zai kara bafa kyakyawan sakamako fiye da farko !

To da karshe bari mu **basu koyaswa** – watau cikakar ma'ana da ainahin bishara, karanta tsarin Allah kan pannin ceto, saukakakiyar hanyar raba bishara tare da bada shaida, wadansu kalubalai da suka shafi bishara tare da yadda za a sha kansu, da dai sauransu. To a yanzu muna cikin ginarda karfafan masu wa'azi!

Wannan karamin misali na nuna ikonda ke tare shiryasda cikaken tsari wanda ya hada wadannan abubuwa hudu. To haka ne rayuka ke canzawa, ga yadda kuna ake gina masu jagoranci!

To haka ne idan nuna son gina wadannan harufa biyar dukansu (Kristi, Al'uma, Halaya, Kira da Kwarewa) a cikin rayuwar jagora, to lalle sai tsara shiri domin ginuwar jagora wanda ya kumshi wadannan sassa hudu na canji (ruhaniya, hulda, koya ta hanyar aiwatawa, da koyaswa). Ba paninda ya kamata a yi watsi da shi!

Wannan shi ne taikacin sanfarin SadaRwa domin ginin Jagora Krista – Bunkasarda KAHKK ta hanayar ruhaniya, hulda, koya, koyaswa

**LeaderSource SGA**

513 South Main St., Suite 2.
Elkhart, IN 46516

Tel: +1 844 532 3371

Email: info@leadersource.org
Website: www.leadersource.org